# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na shida: Neman waraka


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Precious: | 'yar shekara 30 |
| Malama Talatu: | 'yar shekara 45 |
| Julie: | 'yar shekara 40 |
| Tanko: | ɗan shekara 45 |
| Fati: | 'yar shekara 16 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda yake zuwa muku a kan cin zarafin 'ya'ya mata da kuma yi musu fyaɗe a nahiyar Afirka. Wannan shi ne shiri na shida a cikin jerin shirye-shiryen da muke kawo muku. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda Hadiza ta je caji ofis don ta ba da rahoton irin abin da ya faru da ita, amma sai ta yi karo da wani ɗan sanda wanda ya nuna rashin damuwa da halin da samu kanta a ciki. Sherifat, mahaifiyar Fati, ta kai wa Fati ziyara a makaranta. Ta kasance cikin matuƙar farin ciki da irin ƙoƙarin da Fati take yi, har ya sa ba ta gane halin da 'yarta take ciki. A wani ɓangaren kuma, Mrs. Audu ko Malama Talatu, malamar Adams, ta gwada shi da wasu tambayoyi don ta gane abin da ke damunshi. Ina labarin zai kai mu daga nan? Ku biyo mu domin jin amsa a cikin shirin namu na yau mai taken "Neman waraka". Za mu faro ne daga makarantar su Adams, inda Malama Malama Talatu ta aika cewa tana son ganin mahaifiyar Adams ɗin don su tattauna a kan wani abu.

**Fitowa ta 1: A makarantar su Adams**

**Precious:** To, Malama Talatu, kin ce kina nemana, in ce dai lafiya ko?

**Malama Talatu:** To, ban sani ba ko kin lura da yadda halayen Adams suka canza a 'yan kwanakin nan.

**Precious:** Me kike nufi? Wani abu ya faru ne?

**Malama Talatu:** To da ina tunanin za ki gaya min. Maganar ita ce, Adams ya canza sosai. Ba ya son shiga cikin yara 'yan'uwanshi, ko da yaushe sai ki riƙa ganinshi shi ɗaya, kuma bai cika damuwa da ya yi *homework* ɗinshi ba.

**Precious:** To yanzu me kike so in yi a kan wannan? In riƙa yi mai *homework* ɗin ne?

**Malama Talatu:** Yanzu dai Maman Adams zan shawarce ki da ki kwantar da hankalinki. Na yi ɗan ƙoƙarina da zan iya yi don in gano abin da yake damunshi, kuma abin ya sa ni cikin 'yar damuwa.

**Precious:** Da gaske? Me kuma wannan zai iya zama? Kuma muna yi mai duk abin da yake so.

**Malama Talatu:** To ni dai ba zan iya ce miki ga abin da yake damunshi ba, amma ga dukkanin alamu da kuma irin yadda na san Adams, na san cewa akwai abin da yake damunshi. Kuma ko ma dai mene ne, abin ya shafi rayuwarshi sosai.

**Precious:** Yanzu me kike tunanin ya same shi?

**Malama Talatu:** Maman Adams, ba kya ganin cewa ana cin zarafinshi ta hanyar duka... ko kuma ta…

**Precious:** Mene ne? Me ya sa za ki yi mai irin wannan tunanin?! Me kunnena yake ji haka? Kina zargina ke nan da rashin kula da ɗana? Kuma mene ne ɗayan abin? Cin zarafinshi? A'a, a'a, a'a, Malama Talatu, ina ganin kuma fa kin wuce gona da iri. Ba ki da wata dama da za ki zo ki…

**Malama Talatu:** Kalli wannan gwajin da na sa Adams ya yi don in yi ƙoƙarin gano abin da yake faruwa. Dubi irin amsoshin da ya bayar a kan tambayoyin da na yi mishi.

**Precious:** Ba ni in gani! "Me na fi so in yi lokacin da ba na komai?" – "Ba komai." – "Wane ne babban abokina?" – "Ba kowa!" – "Wane ne ba ka so?" – To, ai bai amsa wannan ba.

**Malama Talatu:** Kwarai ya amsa. Idan kika duba za ki ga ya fara rubuta wani abu kuma sai ya goge kwata-kwata.

**Precious:** To, ai wataƙila yana son kowa ne kuma kawai dai ba wanda ya ƙi jini.

**Malama Talatu:** Gaskiya ne Adams yaro ne mai farin jini. Shi ya sa nake ƙoƙarin in taimake shi. Yara kan ji daɗin faɗa maka abin da suke so. ko abin ba sa so, amma daga amsoshin da Adams ya bayar akwai alamun cewa yana ƙoƙarin ɓoye wani abu. Kamar yana tsoron wani abu, ko kuma wani.

**Precious:** Me kuma nake ji haka! Malama Talatu, ni dai na san cewa ke malama ce. Yaushe kuma kika zama mai leƙen asiri?

**Malama Talatu:** Maman Adams, na gane cewa wannan maganar da muke yi na da wuyar gaske a wurinki, kuma ki yi haƙuri na ɗauko maganar. Saboda haka yanzu, Maman Adams, don Allah ki yi tunani: ba wani da kika sani da Adams yake jin tsoro sosai? Wataƙila wani yaro a gida? Wataƙila ma babba ne?

**Precious:** A'a! Adams na zaune lafiya da kawunshi Jammo. A halin gaskiya ma tun da Kawu Jammo ya zo ya fara zama nr yaron ya zama mai ladabi sosai ba kamar da ba.

**Malama Talatu:** Na san cewa maganar da zan gaya miki za ta iya zama miki wata iri, sannan kuma wataƙila ba za ta zama hakan ba, amma ina roƙonki da ki bincika ki gani ko Kawu Jammo, ko ma wane na cin zarafin ɗanki.

**Precious:** Wannan ai hauka ne! Kin yi hauka! Ko dai kin fita daga cikin hankalinki, ko kuma dai kina kishi kawai! Madam Talatu, sai an jima. Nan gaba zan buƙaci da ki mai da

hankali a kan aikinki wanda shi ne koyar da yarona!

**Mai ba da labari:**

Da ma dai yana da wuya mutum ya yarda da irin waɗannan abubuwan da ke faruwa. Amma kuma ba dalili ba ne da zai sa a yi kunnen uwar shegu da su. Me zai faru da Precious saboda wannan mataki da ta ɗauka na nuna halin ko-oho? Nan ba da daɗewa ba za mu ji.

Amma yanzu bari mu koma wata makaranta, makarantar kwanan su Fati, wato Mai Aduwa, inda Julie da 'yan ƙungiyar nan tata da ke yaƙi da cin zarafi suka je don yi wa 'yan makarantar jawabi a kan wannan batu na cin zarafi da fyaɗe da ke da cin rai.

**Fitowa ta 2: A makarantar su Fati**

**Tanko:** Kai, kai, ya isa! Ku yi shiru! Na ce ya isa, ku yi shiru! Ba na so in ƙara jin surutun kowa a ɗakin taron nan. … To, kamar yadda kuka sani, *principal* dai yana hutu, saboda haka ni ne nake kula da makarantar nan a yanzu. To yau muna da baƙi ne da suka zo don su yi mana jawabi a kan wani muhimmin al'amari. Ina son kowa ya mai da hankali a kan jawabin da za su yi. Kuma ku tuna cewa ina kallonku don in tabbatar da cewa kun mai da hankali. Madam Julie, gare ki.

**Julie:** Na gode Malam Tanko, kuma na gode da kowa ya samu halartar wannan taro. To kamar dai yadda kuka ji, sunana Julie, kuma da ni da abokin aikina mun zo nan ne don mu yi muku bayani a kan fyaɗe. … Yauwa. To tun da yanzu mun samu hankalinku, sai mu mai da hankali. Mun zo ne don mu yi muku bayani a kan fyaɗe. Akwai wani a nan da ya san abin da ake nufi da fyaɗe?

To, a sauƙaƙe dai, fyaɗe shi ne dukkan wani nau'i na yin jima'i ba tare da amincewa ba, ko kuma an tilasta amincewar. Wannan na iya shafar kowa, amma abin ya fi shafi shafar mata. Yawanci waɗanda suke aikata wannan aika-aika kan kasance waɗanda aka sani ne, ko kuma ɗan'uwa. Yana iya zama aboki, ko wanda kuke aji ɗaya, ko maƙwabci, ko wani da ake da dangantaka da shi, ko ma wani malami. … Kwarai. Na san cewa wani abu ne da zai yi wuya a yarda da shi, amma yana faruwa sosai, kuma ya kamata mu tattauna a kansa. To, akwai nau'i dabam-dabam na fyaɗe, kuma ba dukkansu ba ne suke kasancewa sai an sadu tsakanin wanda abin ya shafa, da kuma mai aikata cin zarafin. Misali, taɓa jikin mace, yi wa mutum barazana, leƙe, duk ba tare da amincewa ba.

To amma dai, ba mun zo nan ba ne don mu zargi wani. Muna so ne kawai ku gane abin da ake nufi da keta haƙƙin wani ta hanyar fyaɗe ta ko wane irin hali, saboda ku taimaka mana wajen hana aukuwar hakan. Bincike yana nuna cewa, ana tilasta wa mata yin jima'i ne a karonsu na farko na sanin ɗa namiji. Amma ba a kai rahoton aukuwar hakan saboda waɗanda abin ya faru da su suna tsoron kai rahoton, ko kuma suna jin kunyar kai rahoton abin da ya faru da su ga jami'an 'yan sanda, ko kuma su faɗawa ƙawayensu, ko 'yan'uwansu a kan cin zarafin da aka yi musu.

**Tanko:** Ki yi haƙuri! ba na yi niyyar na tsai da ke ba ne. Kina iya ci gaba.

**Julie:** Muna so mu ba da ƙwarin gwiwar cewa kada ku ji tsoro, kuma ku tashi ku yaƙi cin zarafin 'ya'ya mata!

**Mai ba da labari:**

Daga nan kuma sai Julie da abokanta suka kama hanyar fita daga ɗakin taron zuwa inda motarsu take. Za su ja motar su tafi ke nan, sai ga Fati ta taho a guje don ta iske su.

**Fati:** Malama Julie, ki tsaya don Allah! Don Allah ki tsaya! Kar ki tafi! Kar ki tafi! …

**Mai gabatarwa:**

Da wannan kuka na Fati muka kawo ƙarshen shirin na yau. Me zai faru a gaba? Shin Fati za ta iya samun ƙarfin zuciyar faɗa wa Julie abin da ya same ta bayan wannan shi ne karo na farko da ta haɗu da ita? A kasance da mu a shiri na gaba domin jin amsa. Amma za a iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe domin ƙara sauraron wannan shirin. Ana iya haɗewa da mu a shafinmu na Facebook domin yin muhawara ko a aiko da saƙo. Ku huta lafiya, sai mun sadu a shiri na gaba.